https://www.al-feqh.com/ha

# Wajiban Umara

## 1. Sanya Ihrami daga miƙati,

saboda faɗin Manzon Allah (S.A.W) bayan ya faɗi wuraren miƙati ya ce, «Waɗannan miƙatan na mutane garin ne, da waɗanda suka zo da hanyarsu, ga wanda yake da niyyar hajji da umara»

## 2. Aske kai gabaɗaya ko saisaye,

saboda faɗin Allah Maɗaukakin Sarki :{Tabbas zaku shiga masallacin harami – in sha Allahu – kuna masu aske kanku gabaɗaya k. o kuna masu saisaye}[Al-fathu : 27].

# Sunnonin Umara

Duk abin da ba rukuni ko wajibi ba, to sunna ne, kamar abubuwan da za su zo :

1. Yin wanka yayin sanya ihrami

2. Yin ihrami da kwarjalle da mayafi farare.

3. Yin talbiyya da ɗaga murya da ita.

4. Yaye kafaɗar dama a wajen ɗawafi, shi ne sanya mayafi ƙarƙashin hammatar hannun dama.

# Faɗakarwa:

1. Wanda ya bar rukuni daga cikin rukunan umara, umararsa ba ta yi ba, har sai ya zo da shi.

2. wanda ya bar wajibi daga cikin wajiban umara, to wajibi ne a kansa ya yi yanka, (wato ya yanka akuya, ko ya ba da ɗaya bisa bakwai na saniya ko raƙumi)

3. Wanda ya bar sunna daga cikin sunnonin umara babu komai a kansa, umararsa ta inganta.



Ihrami



Aski Da Saisaye

